*KASHI NA DAYA HALITTA*

Darasi na 1

# YADDA AKA HALICCI DUNIYA

Farawa 1:1-25; 2:1-3

# SHIRIN MALAMI

**Kafa Harsashi mai Karfi: Allah Mai iko Dukka.**



**ME MUKE SO YARA SU KOYA A WANNAN DARASI?**

Za su:

* gane cewa Allah madawwami ne, kuma ba shi da farko ko karshe.
* koya cewa halittar duniya da Allah ya yi ya nuna cewa shi Mai Iko Dukka ne.

**HADDACEWA**

"Kafin a kafa tuddai, kafin kuma ka sa duniya ta kasance, kai Allah ne, madawwami."

Zabura 90:2

### *ZARARIN LITTAFI MAI TSARKI*

Darussa da yawa a wannan shekara za su bayyana mana wata muhimmiyar gaskiya game da Allah. Koyon wadannan gaskiya game da Allah za su ***kafa harsashi mai karfi*** domin wasu gakiyan da za mu so yara su koya. A kowane mako, ka karfafa yara su yi tunani a kan wani halin Allah, su kuma roke shi ya taimake su don su kara saninsa sosai. (Dubi shafi 4 domin Karin ba-yani a kan wannan.)

Darussa biyu na farko suna kan halittar duniya da Allah ya yi. Yi amfani da su don ka koya wa yara cewa Allah Mai Iko Dukka ne.

Allah ya halicci tsire –tsire, kifaye, tsuntsaye da dabbobi masu launi iri-iri da siffofi dabam-dabam, da kuma kanci iri-iri.
Allah ya halicci su domin mutum ya ji dadinsu. Mutum shi ne halitta na karshe, halitta mafi ban mamaki. Halitta tana koya mana cewa Allah mai kauna ne, shi cikakke ne, mai hikima ne shi, kuma Shi Mai Iko Dukka.

### *ME AKE BUKAT DOMIN DARASIN NAN?*

1. Hoto na 1. "Murnar Halitta" domin KARSHEN DARASI.

2. Domin Labari Daga Littafi Mai Tsarki (kashi na 1-4), dubi shafi 6 domin a zana Ranakun Halitta. Ka zana naka babba saboda ka nuna yayin da kana magana a kan abin da ya faru a kowace rana. Ajiye su don maimaici.



**Gabatarwa**

## LOKACIN DARASI

**A FARA DA ADDU'A**

♦ RAIRA waka a kan yadda Allah ya halicci duniya ko a kan girman Allah.

♦ TAMBAYOYIN da za ka yi:

Aya ta fari a Littafi Mai Tsarki ta fara da "A cikin farko *…" Yaushe ne farkon?* (Farkon shi ne lokacin da ba a halicci kome ba. Yana da wuya mu gane saboda bamu san lokaci kamar haka ba.)

*Wanene yake nan a farko?* (Allah)

Ashe Allah tsoho ne sosai. *A tunaninka shekarun Allah nawa?* (Allah ba shi da shekaru. Ya kasance a dukan lokaci.)

♦ FADA —Yau za mu yi Magana ne a kan "kafin farko." Za mu yi Magana kuma a kan abin da ya faru.

## 1. A cikin farko (aya 1)

- FADA — Kalmomi na fari a Littafi Mai Tsarki sun fada mana wani abu game da Allah da wani abu game da farko. Kafin farko: Babu duniya, babu mala'iku, babu dabbobi, babu sararin sama, babu iblis, babu tsuntsaye, babu teku, babu mutane, babu tsire-tsire. Duk abin da muke gani kuma muka sani suna da farko, sai Allah da kansa. Yana nan a kowace lokaci. Babu lokacin da za a ce Allah baya nan.
- KARANTA Fara 1:1 "A cikin farko Allah ya halicci sama da kasa." Ka san ma'anar halitta? Halitta ita ce a yi wani abu. Bari mu dubi abuwan da Allah ya halitta. Lokacin da Allah ya halicci sama da kasa, ba da wani ya halicce su ba!
- Malami: NUNA zane na Rana ta 1. (Dubi "Me Ake Bukata?")

## 2. Rana ta 1 ta 2 (aya. 1-8)

- FADA — Abu na fari da Allah ya yi bayan ya halicci duniya shi ne haske. Kafin Allah ya halicci haske babu kome.
- TATTAUNA — Me ya sa yana da taimako gare mu mu sami haske kuma mu sami duhu kowace rana?
- FADA — Abu na biyu da Allah ya halitta shi ne sararin sama. Yanzu akwai sarari tsakanin ruwa na duniya da sama.
- NUNA zane na Rana 2.

## 3. Rana ta 3 ta 4 (aya 9-19)

- FADA —Allah ya sa ruwaye su kasance tare don su zama tekuna da kuguna. Yanzu akwai busasshiyar kasa. Allah ya kira busasshiyar kasar duniya!
- BAYYANA—Allah yana so tsire-tsire da itatuwa su yi yawa a duniya don haka ya sa su su girma su yi 'ya'ya. Tsire-tsire da itatuwa suna ba mu abinci, suna bamu inuwa, suna ba mu furanni masu kyan gani.
- NUNA zane na Rana ta 3
- FADA—Allah ya yi haske da sama saboda su bamu rana da dare. Suna kuma ba mu lokacin ruwa da kaka, da makonni da watanni da shekaru. Rana shi ne babban hasken da Allah ya halitta ya ba da haske da rana. *Wadanne ne hasken masu ba da haske da dare?* (Wata da taurari.)

## 4. Rana ta 5 zuwa 7 (aya 20-25; 2:1-3)

- FADA—Yanzu lokaci ne da Allah zai yi rayayyun halittu. Ya yi kifi da tsuntsaye. Allah ya yi kifaye da tsuntsaye iri-iri. Muna jin dadin wakokin tsuntsaye, muna ganinsu suna firiya, wasun kuma muna cinsu.
- NUNA zanen Rana ta 5.
- Yi Magana a kan dabbobi na kasa iri-iri wadanda Allah ya yi su. Ya yi manyan dabbobi, da kananan dabbobi, da wasu kwari, tururuwa, kudaje da su sauro. *Wadanne ne wasu dabbobin da muna cin su? Wadanne ne dabbobi ne suna yi mana aiki?*
- NUNA zane na Rana ta 6.
- FADA—A makon gobe ne za mu kara ji game da halittar mutum wanda Allah ya yi.
- KARANTA Farawa 2:2-3. Allah ya gama aikin halitta don haka a kan rana ta 7 ya huta daga aikinsa.

## Karshen Darasi ...

► **Koyar da Haddacewa yanzu (Zabura 90:2).**
TAMBAYA—*Me ayan nan ta tuna mana game da Allah?* (Allah madawwami ne). Yana da rai tun kafin a fara kome kuma a ko yaushe yana nan. Allah ya halicci duniya. Wannan yana tuna mana cewa shi Mai Iko Dukka ne.
TATTAUNA—*Idan mun tuna cewa Allah mai iko dukka, shi kuma madawwami ne, yaya wannan yake shafan rayuwarmu?*
FADA—Idan ka ga abubuwan da Allah ya halitta a wannan mako, ka tuna abin da muka koya game da Allah. Ka sami lokaci ka gode masa saboda shi dawwamame ne, shi kuma mai iko dukka ne.

* **Ayyuka:** KARANTA wakar 'Murnar Halitta' (Hoto na 1) da hankali. FADI wasu abubuwan da wakar ta fada mana wadanda Allah ya halicce su.

**ADDU'A:** Yara biyar ko shida su yi addu'a suna gode wa Allah saboda abu daya da ya halitta. Mu gode masa saboda wadannan abubuwa suna tuna mana cewa shi Mai Iko Dukka ne, shi kuma madawwami ne.

**WAKA:** "Abu duk a duniya Ubanmu ne ya yi ..." ♫

**Kafa Harsashi mai Karfi:** *Allah Mai Iko Dukka.* (Dubi shafi 4 game da wannan koyarwa.)